## EPISODE 18

**Characters**

*Alhaji Bature*

*Laraba*

*Dr. Daoud*

*Hannah*

*Tina*

*Danjuma*

---

**Scene 1**

**Northern Kaduna, Alhaji Bature's shop.**

| | | |
|---|---|---|
| 1. | **MUSIC:** | **THEME MUSIC** |
| 2. | **SFX:** | **DISTANT SOUND OF VEHICLES AND MOTORCYCLES PASSING.** |
| 3. | **LARABA:** | *Assalamu alaikum* Alhaji Bature. Yaya kasuwan ya iyali? |
| 4. | **ALH. BATURE:** | *Amin Wa' Laikis Salam* Laraba. Alhamdilla Komai Lafiya lau |
| 5. | **LARABA:** | Madallah, don Allah Alhaji ina son a saida min sabulun wanka, man wanke hakora da tishu fiefa |
| *6.* | **ALH. BATURE:** | toh ai sai ki zabo sabulun wankan daki ke so, tunda ina da kaloli dabam dabam kuma na san mata da zabe. |
| *7.* | **LARABA:** | **(LAUGHING)** Ba dukan mu bane ke zabe fa, ni a bani kowace ma |
| *8.* | **SFX:** | **SOUND OF NYLON BAG RUSTTLING.** |
| *9.* | **LARABA:** | Alhaji mun gode da gudumawar da ka bayar a taron da muka yin a karshe na kungiyar lafiyar al'uma. Hakika ka saukaka mana abubuwa daka yi alkawarin magana da duk wani mai fada aji karamar hukumar . |

| | | |
|---|---|---|
| *10.* | **SFX:** | **<u>SOUND OF RANDOM PROVISIONS BEING REARRANGED</u>.** |
| *11.* | **LARABA:** | *Toh* Alhaji, ina ganin abubuwa sun yi maka yawa, don Allah nawa ne kudin? |
| *12.* | **SFX:** | **<u>SOUND OF RANDOM PROVISIONS BEING REARRANGED CONTINUES</u>** |
| *13.* | **LARABA:** | Alhaji? Alhaji Bature. Lafiya kuwa? Ina ta Magana amman hankalin ka baya nan.. |
| 14. | **ALH. BATURE:** | **(ALMOST SPRINGING UP)** E ina jin ki. Ina kokarin in shirya kayakin nan ne. amma ba komai lafiya lau |
| 15. | **LARABA:** | **(LAUGHS GENTLY)** Alhaji, akwai da matsala, ina ta tabbayar ka nawa ne nawa ne domin in biya amma sam baka ji ni ba |
| 16. | **ALH. BATURE:** | **(LAUGHS HALF-HEARTEDLY)** Ah nars Laraba, kyali ne kawai hankali na baya nan, kada ki damu da biya, ai kina taimaka ma al'umar nan sosai, haba dan kayan nan? |
| 17. | **LARABA:** | Ah Alhaji Bature, ba za ayi haka ba |
| 18. | **ALH. BATURE:** | a'a ba matsala, kyale kawai |
| 19. | **LARABA:** | toh Alhaji, nagode kwarai, ni na tafi |
| 20. | **ALH. BATURE:** | **(HESITANT)** Nan jira kadan nars Laraba, ina son in tabbaye ki sharawa da zan ba aboki na |
| 21. | **LARABA:** | Ba matsalla Alhaji, menene shawarar da kake bukata? |
| 22. | **ALH. BATURE:** | **(CLEARS THROAT)** Nars Laraba, idan likitoci sun gwada matar aboki na cewar zata iya samun juna biyu, amma har yanzu bata samu ciki ba menene zai iya kasancewa matsallar? |
| 23. | **LARABA:** | Toh, ya dace ace maigidan ya bi matar zuwa gwajin shi ma. Hakan za'a gane ko shi ke matsallar. Ko shi ma yayi gwajin ne? |
| 24. | **ALH. BATURE:** | A'a bai yi gwajin ba, yace yana da yikinin lafiyar sa, kuma yana ma da wasu yaran, |

25. **LARABA:** *Toh,*idan haka ne, zan shawarce ka da ka fada wa abokin ka ya tattauna da dukan matansa ba tare da boye-boye ba, sai kuma shi da matar su je domin Karin bayani a bangaren tazarar haihuwa na asibitin

26. **ALH. BATURE:** Toh. Ehn amma yaya za ace shi ke da matsala?

27. **LARABA:** Hmm, Alhaji Bature, ba matsala bace ko abin laifi, damar ai ya chanchanta ma'aurata su yi himar tattaunawa a tsakanin su, ko wajen neman juna biyu ko tattauna game da yawan yara da suke son su samu.

28. **ALH. BATURE:** Haka ne

29. **LARABA:** Hakan zai sa su bada dukan bayanan da ake bukata. Kuma zai taimaka ma maaikatan asibitin wajen sanin shawara da ta dace su dauka.

30. **ALH. BATURE:** Na'am, na gani. Amma za a same mafita ma wannan abokin nawa?

31. **LARABA:** Mai yiwane. Ni dai ina kan baka nan a ka shawarci abokin ka da ya je asibiti don abashi kwararran shawara, anan za su san abunda ta dace ayi.

32. **ALH. BATURE:** Yayi ainun, nagode kwarai, zan je in ga Dacta Daoud.

33. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Scene 2**

**Northern Kaduna. Danjuma's House. Late Afternoon.**

34. **SFX:** **<u>SOUND OF DOOR OPENING AND CLOSING.</u>**

35. **TINA:** Barka da dawowa, yaya Danjuma.

36. **DANJUMA:** **(COMING ON MIC)** Barkan ki, me kike yi a gida ke kadai, kuma ina yar ki Hannah?

*37.* **TINA:** Ta fita, amma bata fada min inda zata ba ko yaushe zata dawo ba..

| | | |
|---|---|---|
| 38. | **DANJUMA:** | **(SMILING)** Tina *kenan*. Na sam tafi ta ziyarci babbar ta ne, nayi zaton ta dawo ne sai yasa na tabbaye ki, amma ba komai nagode da sanarwan |
| 39. | **TINA:** | Bara in kawo maka abincin ka tunda a gama girkawa. |
| 40. | **SFX:** | **SOUND OF SHUFFLED FEETS AS TINA MAKES TO LEAVE** |
| 41. | **DANJUMA:** | Tina, ki san dai kullun ina jiran matata har ta dawo kafin in chi abinci na. |
| 42. | **TINA:** | **(CUTS IN)** Amma ita ce ta girka abinci ba nice ba. Kawai ce min tayi in zuba maka idan ka dawo. Don Allah kada ka sa ni cikin matsallar ta kuma saboda rashin yin abinda ta umurce ni. |
| 43. | **DANJUMA:** | hmmmm Tina, shirya min a tibirin. |
| 44. | **TINA:** | **(HAPPILY)** Ai na riga da na shirya maka, abincin na cikin flask, kawai ci zaka yi |
| 45. | **SFX:** | **SOUND OF FOOD BEING DISHED INTO A PLATE IN A PLATE** |
| 46. | **SFX:** | **SOUND OF SPOON SCRAPING PLATE AS DANJUMA EATS.** |
| 47. | **DANJUMA:** | **(DISGUSTED)** Tina, menene yasa abincin ke dandano haka?! |
| 48. | **TINA:** | Menene, ba dadi ne? |
| 49. | **DANJUMA**: | A’a, bana jin dadin dandanon, yana yi min wani iri |
| 50. | **TINA:** | Toh, ban sani ba fa, ai na fada maka cewa yaya Hannah ce ta girka abincin. Kilar tayi amfani da saben kayan kamshi da kuma saben sinadaren girki, ko kuma wanda take amfani da su amman suyi yawa |
| 51. | **DANJUMA:** | **(GROGGY)** Toh koma menene, bana jin dadi **(PAUSES)** tina, ina mugun jin barci, kamar bani da lafiya ma. Ina ganin zany i barci a kujerar nan fa |

| | | |
|---|---|---|
| 52. | **TINA:** | **(FAKING CONCERN)** Eyyah! Sannu, dan jingina a kan kujeran kadan, kayi hankali.. |
| 53. | **SFX:** | **SOUND OF DANJUMA COLLAPSING WITH SOFT THUD TO THE GROUND.** |
| 54. | **TINA:** | **(LAUGHING WICKEDLY)** Yanzu bara mu gani ko waye maigidan. Wato Hannah tana ganin cewa it ace ke da wayon samun miji na kwarai, eh? Toh zata gane cewa nima ina da hikima |
| 55. | **SFX:** | **SOUND OF DANJUMA'S FEET BEING DRAGGED ON THE FLOOR BY TINA.** |
| 56. | **TINA:** | **(PANTING)** Heh Danjuma na da nauyi fiye da yadda nake tsamani **(PAUSING)** Kai ashe jan mutun a kan baranda haka da wuya. **(PAUSING)** Koda yake na tabbatar bazai tashi yanzu ba, tunda na sanya masa kwayoyi barci cikin abincin sa |
| 57. | **SFX:** | **SOUND OF DANJUMA'S FEET STILL DRAGGING. SOUND OF DOOR OPENING.** |
| 58. | **TINA:** | **(STILL PANTING)** idan na gama abinda na shirya wato na kwantar da Danjuma akan gado in kuma kwanta agefen sa, in Hannah ta dawo ta ganmu tare, zan zama matar Danjuma Giwa ai kawai **(LAUGHS WICKEDLY)** saida bukatan in zama mai larlashin sa kaiwai |
| 59. | **SFX:** | **SOUND OF DANJUMA BEING LIFTED AND DROPPED ON THE BED.** |
| 60. | **TINA:** | **(PANTING HEAVILY)** Heh dubi yadda nake zufa. Toh yanzu na kwantar da Danjuma akan gadon, sauran in nemo kayan barcin Hannah in sanya, ai zata gani yau |
| 61. | **SFX:** | **SOUND OF WARDROBE DOOR/DRAWER BEING OPENED.** |
| 62. | **TINA:** | **(HAPPILY)** Yauwa!, komai yayi daidai. Idan Hannah ta ga wannan, Danjuma zai zama maigida na. |
| 63. | **MUSIC:** | **BRIDGE MUSIC** |

**Scene 3**

**Northern Kaduna. Hajiya Inna's House: Exterior. Evening.**

| | | |
|---|---|---|
| 64. | **SFX:** | **<u>SOUNDS OF ROAD AMBIENCE.</u>** |
| 65. | **DR. DAOUD:** | **(CONCERNED)** *Haba* Laraba! Ina ta magana tun dazu, amma kamar baki son ki amsa ni, menene ke damun ki, kiyi min magana mana. |
| 66. | **LARABA:** | Daoud ba komai, ina dan jin ciwon kai ne |
| 67. | **DR. DAOUD:** | **(DISAGREES)** sam, ba ciwon kai ne zai kasance dalilin da baza ki kula nib a, duk da cewa ina magana akan burin rayuwar mu, tabbas akwai wani abun |
| 68. | **LARABA:** | Ba wani abu fa, kada dai san yadda ciwon kai yake, wani sayin zai sa mutun yaji kamar rashin lafiya sosai |
| 69. | **DR.** DAOUD: | Na sani Laraba, amman wannan ba shine farkon yin hakan baa i, har ma ta kai yanzu kina guje min a asibiti, kin guje min tun da na fada miki abinda faru da matata. |
| 70. | **LARABA:** | **(DEFENSIVE)** don Allah Dacta kar bar zancen nan haka, na fada maka lafiyata, ciwon kai ne kawai kuma yau bana jin yin magana |
| 71. | **DR. DAOUD:** | *Haba* Laraba! Don Allah kada ki kyale ni a duhu, nasan saboda abinda na fada miki ne, don Allah kice wanni abu domin mu fahimci juna |
| 72. | **LARABA:** | Dacta Daoud don Allah ka kyale ne…. |
| 73. | **DR.** DAOUD: | **(CONFUSED, UPSET)** In Kyale ki?! Tayaya?! Don Allah me keki nufi da hakan? Ko dai wata matsalar ce daban wanda ban san da it aba? Ko dai kina nufin ina damun ki ne? |
| 74. | **LARABA:** | Ni ban san abinda kake nufi ba. Ni dai na gaya maka abinda ke damuna. Ina son in koma cikin gida. |
| 75. | **DR. DAOUD:** | **(UPSET)** Ni kuma ki bar ne haka a rude? Haba Laraba! |

| | | |
|---|---|---|
| 76. | **LARABA:** | **(COLDLY)** Dacta zan koma cikin gida, nag ode da ziyara, sai anjima |
| 77. | **DR. DAOUD:** | (**SERIOUS, UPSET**) Me keki son ki yi? Don Allah kada ki tafi muna cikin magana, yanzu nagane! Kina ganin laifi nani hatsarin da ta sa mutuwar iyali na ko? |
| 78. | **LARABA:** | Ni ban ce haka ba. |
| 79. | **DR. DAOUD:** | Laraba, ba sai kin fad aba ai. Kin dauke min tun rannar da na gaya miki. Idan ba haka ba me kike nufi da yadda kike yi? E? ki gaya mini . |
| 80. | **LARABA:** | **(SHOCKED)** Menene?! Don Allah kada ka dawo da zance kuma. Abin bakin ciki ne ai kuma ta riga ta wuce. Bana son ta haifar da wani bakin cikin. |
| 81. | **DR. DAOUD:** | Toh naji. **(CALMLY)** Don Allah kifada min gaskiya, kina ganin laifina ni mutuwar matata da dahna?. |
| 82. | **LARABA:** | **(INDIFFERENT)** Na fahimci cewar a rayuwa akwai wasu mutanin da ke da rashin sa'a, rashin rabo da bakin jinni, duk ida suke akwai tashin hankali. Ba zan iya zama tare da irin mutanen nan ba,. |
| 83. | **DR. DAOUD:** | **(UPSET)** Abin da kike gaya min kenan? Laraba neni fa daoud din ki. Kina nufin zaki rabu dani akan laifin da ba nawa ba? Akan abinda bani da iko akai? |
| 84. | **LARABA:** | **(COLDLY)** Kayi hakuri dacta, Ba abinda zan iya yi, kayi hakuri. |
| 85. | **DR. DAOUD:** | **(UPSET)** Toh Laraba, gaskiya ba dalilin cingaba. Idan har zaki zarge ne da laifin da bani da iko akai. Sai anjima. |
| 86. | **MUSIC:** | <u>**BRIDGE MUSIC**</u> |

**Scene 4**

**Northern Kaduna. Danjuma's House. Late Afternoon.**

87. **SFX:** **<u>SOUND OF DOOR OPENS AND CLOSES AS TINA WALKS OUT OF DANJUMA'S ROOM</u>**

88. **HANNAH:** **(SHOCKED)** Me nake gani?! Tina! Me kike yi a daki na? har da sa kayan barci na?!

89. **TINA:** **(CASUALLY)** Oh! Hannah! Kin dawo? Barka da dawowa.

90. **HANNAH:** Baki bani ansa ba Tina. Na tambaye ki me kike yi a daki na sanye da kayan barci na. kina nufin yanzu dakin maigidana ya zama miki kamar saurar dakuna da kike shiga da fita acikin gidan nan?

91. **TINA:** Don Allah ki rage muryar ki. Akan menene kike ihu? Daki ne fa kamar wata kayan gabas.

92. **HANNAH:** **(SURPRISED)** dani kike? Tina! Yanshe kika yi kaurin yuwa haka? Wannan halin taki sai karuwa take, kuma Allah ma yasan na gaji, bazan iya ba.

93. **TINA:** Oh, haba? Toh me za kiyi game da hakan?

94. **HANNAH:** Ina son ki je ki kwashe dukan kayanki ki bar min gida yanzu nan. Na gaji da irin wannan renin.

95. **TINA:** **(SMILING)** Hannah, baki da dama ko kadan da za ki iya korina daga gidan nan, ba hurumin ki bane. Wanda ke da damar shine Danjuma, idan kuma bai ce hakan b aba ida zani

96. **HANNAH:** **(FURIOUS)** Toh, har ta kai haka Tina? Toh zan kira wanda suka dace su gaya miki ki bar gidan su fada miki.

97. **SFX:** **<u>SOUND OF PRESSING THE PHONE'S BUTTONS TO DIAL A NUMBER</u>.**

98. **HANNAH:** Idan na kira Mama da Danjuma, suka zo, za mu san wa zai bar gida ma wani….

99. **TINA:** Wani danjuma kike kira? Wanda ki gida tun dazu? **(WICKEDLY)** yar uwata, ba sai kin bata lokacin ki ba, saboda yana kwanci a dakin sa.

| | | |
|---|---|---|
| 100. | **HANNAH:** | **(SHOCKED)** Me kika ce?! Yana ma cikin gidan amma kina da karfin giwan shiga dakin? Har da sa kayan nan!!! Wayyo Allah na ! Tina menene kika maida kanki? |
| 101. | **TINA:** | **(LAUGHING)** Kai Hannah!, kina bani mamaki wallahi!. |
| 102. | **HANNAH:** | **(ANGRILY)** Ina mijina? Ina danjuma? |
| 103. | **LARABA:** | **(STILL LAUGHING)** Ki kwantar da hankalin ki yar'uwata, mijinki na kwance a dakin sa, yana hutawa. |
| 104. | **HANNAH:** | **(CONFUSED, ANGRY)** don me kike karya akan mijina haka? Tina! Mun karbe ki cikin gidan mu, mun baki wurin zama amma haka zaki saka mana? |
| 105. | **TINA:** | Daman ni Danjuma naki so. Shine nake saurayin da nake fada miki. Wanda nace miki abokin aiki na din nan. |
| 106. | **HANNAH:** | **(ANGRILY)** Makaryaciya. Danjuma baza taba aikata haka ba. Yafi karfin haka. |
| 107. | **TINA:** | **(LAUGHS MOCKINGLY)** Idan so samu ne ba! Toh yar'uwata ni da danjuma muna cikin kogin soyayya mai dadi yanzu. |
| 108. | **HANNAH:** | **(CONFUSED, CLOSE TO TEARS)** karya kike, sam bazai iyu ba. Nasan karya kike, danjuma na bazai taba cin amanata ba |
| 109. | **TINA:** | **(CONFIDENT)** Toh Hannah, idan baki yarda dani ba, ki shiga daki ki duba mana. Amma don Allah banda ihu, saboda Danjuma, agajiye yake yanzu kuma yana hutawa |
| 110. | **SFX:** | **<u>SOUND OF HANNAH'S HURRIED FOOTSTEPS BACK TO DANJUMA'S ROOM. DOOR OPENS.</u>** |
| 111. | **HANNAH:** | **(SHOCKED)** Wayooooo Allah!!! Menene haka?!!! **(SHAKING DANJUMA FURIOUSLY)** Danjuma tashi. Danjuma. Wani irin barcin karya ne haka! Danjuma ka maida ni sakarya ne ko? |
| 112. | **TINA:** | Ki Hannah! Baki san lokacin da mutun ya gaje kuma yana bukatan hutu bane? Kina dai ganin danjuma ya gaji kwarai, |

kuma baya jin yi miki magana, saboda haka ki rike girman ki ki tafi, kada ki jawo tashin hankali anan. Don Allah. .

113. **HANNAH:** **(SCREAMING)** Tina Kina hauka! Fita daga gida na!

114. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**